KUNDIN TSARIN MULKIN JUNHURIYAR NIJERIYA

"Nigerian Constitution"

Kwance -Tushen NIJERIYA

Bldr. Ibrahim Muhammad Dankyauri

Abubuwan da ke ciki

1) Gabatarwa,.....3

2) Asalinsa.....5

3) Me wannan kundin na ƙarshe ya ƙunsa?....10

4) Ina mafita?.....20

5) Kammalawa…….....23

_____ ///_____

1) Gabatarwa

Allah Ya ƙaddara mana zama cikin ƙasa ɗaya saboda wani dalili ba lallai mu san shi ba.

Kafin zuwan Turawan mulkin mallaka, mutanen dake zaune cikin ƙasar da ake kira yau da suna Nijeriya ba haɗe suke ba. Kowanne ɓangare nada yarensa, al'adarsa da Addininsa da irin shugabancinsa. Duk da cewar Yaren da muke da su a Nijeriya, sun doshi 300 da ɗoriya, wannan bai hana mu cuɗanya da juna ba. Domin a nan Arewa kusan kowa na jin Yaren Hausa, Fulaninmu da Barebarinmu, zuwa su Margi, Kare-Kare, Lunguda, Ɓachama, Gwari, Babur, duk suna jin Hausa.

Mu anan arewa, Turawa sun same mu da tsarin makarantunmu, Addininmu, Al'adar mu da Shugabancinmu. Shari'ar Muslunci ake yi. Babu mashayar giya, babu gidan karuwai babu gidan reful da caca. Wannan kuma ya samo asali da Jihadin Uthman bin Fodio na Jaddada Musulunci inda yake a kafe, da kuma musuluntar da maguzawa da sauran ƙabilun da ba Hausa-Fulani ba.

Zuwan Turawa ke da wuya, sai suka fatattaki sarakunan mu, suka kashe na kashewa suka kori na kora sannan suka rusa duk wani tsarin shugabancin Shari'a irin ta Musulunci wadda Alƙur'ani yazo da ita. Suka hana mu aiki da Alƙur'ani cikin haddi. Gidajen wasanni da giya da karuwai da caca suka yawaita tare da ragowar baɗaloli da sharholiya.

Dokokin gudanar da ƙasa (Constitution) ya koma ƙarƙashin Sarauniyar Ingila wacce ta sa aka tsara su domin biyan buƙatunsu na wawashe dukiyar ƙasa da mayar da ita mallakar su tare da tura ta ƙasar Biritaniya da hanyar jirgin ƙasa da jirgin ruwa. Wannan tasa suka yi hanyar dogo

tun daga Nguru zuwa Kano zuwa Legas da Patakwal. Sun kwashe mana gyaɗa, dabbobi da fatunsu, ƙaro da gabaruwa da sauransu. Haka abin ya kasance har zuwa lokacin da suka bamu yancin kai a shekara ta 1960 miladiyya. Ni ɗin nan mai wannan rubutu an haifeni wajejen ƙarshe-ƙarshen 1959.

Turawa sun haɗe jama'ar da take da al'adu, yare, Addini, tsarin shugabanci da zamantakewa mabanbanta cikin ƙasa ɗaya tare da tilasta musu wani tsarin shugabanci na kafirci -mu a fahimtar mu ta Musulunci. Saboda haka babu ta yadda za a sami ci gaba na haƙiƙa mai ɗorewa. Wannan yana daga abinda ya hana ruwa gudu cikin rayuwar yan Nijeriya, kullum muna cikin azabtarwar shugabanni yan barandan Turawan Mulkin Mallaka.

2) Asalin Kundin Tsarin Mulkin Nijeriya (Origin of Nigerian Constitution).

Kundin Tsarin Shugabancin Nijeriya wadda Nijeriya ta gada daga Turawan Mulkin Mallaka ya samo asali ne tun daga lokacin da Turawan suka duro cikin ƙasashenmu. Bayan sun kame kudu ta yamma (ƙasar Yoruba) da kudu ta gabas (ƙasar Igbo) sai suka kama ƙasar Arewa wadda yawancinsu Hausa da Fulani da Karuni ne. Waɗannan yankuna suka sa musu suna protectorate.

A daidai wannan lokaci Sarauniya Ezzabil I ta umarci mutanen ta da su rubuta "Constitution domin gudanar da mulkin Nijeriya da su Turawan za su yi.

Saboda haka aka rubuta na farko mai suna:

1) Clifford Constitution a shekarar 1922 daga nan sai:
2) Richards Constitution a shekara ta 1946 "Westminster".
3) Macpherson Constitution 1951
4) Lytteton Constitution 1954

Duk waɗannan lokutan, Sarauniyar Ingila itace Shugabar Ƙasa kuma Turawan da ta turo sune Gwamnoni. Bayan an hade protectorate guri guda sun zama ƙasa ɗaya kuma yan rajin karɓar mulkin kai sun yuƙuro, sai Sarauniya ta bada umarnin a sake rubuta wani kundin da zai dace da mutanen mu amma ta ƙarƙashin ƙasa su za mu yiwa hidima. Domin kanmu ba zai haɗu ba ta yadda za su ci gaba da mulkarmu a fakaice.

A shekara ta 1953, anyi wani taro (conference) akan kundin mulkin Nijeriya kuma wakilai shida shida suka halarta daga shiyyoyi uku na Nigeriya tare da ɓangaren Camaroon. Shiyyoyin sune Arewa, Kudu ta gabas da Kudu ta yamma.

A shekara ta 1954, aka ƙirƙirar da Tarayyar Ƙasar Nijeriya "Federation of Nigeria", ƙarƙashin ka'idodi na Tarayya "Federalism". Wannan kuwa ya share hanyar samun yancin kai daga Britaniya. Amma duk da haka Constitution na Lyttleton na 1954 ya bada ƙofa da ta haifar da ɓangaranci ƙwarai a cikin tsarin.

Kundin shekarar 1960

A shekara ta 1960 anyi wani Constitution mai suna "Independence Constitution" wadda Britaniya ta ƙaddamar ga Nijeriya a matsayin ƙasa mai yancin kai, wadda aka fara aiki da shi a ranar 1 ga watan Oktoba 1960.

Karƙashin wannan Constitution, NIJERIYA ta ci gaba da ɗaukar Sarauniya Ezzabil II a matsayin itace Shugabar ƙasar Nijeriya, kuma Dr. Nnamdi Azikwe ya wakilceta a matsayin "GOVERNOR - GENERAL.

Kundin shekarar 1963

Kundin Tsarin mulki na biyu (1963) ga Nijeriya ƙasa mai cikakkiyar iko yanzu, ya haramta tsarin masarautar Britaniya kuma ya tabbatar da Junhuriyar Nijeriya ta farko "First Nigeria Republic" ta yadda jama'ar Kasa zasu mulki kansu da kansu. Wannan kundin ya fara aiki ne 1 ga Oktoba 1963 lokacin bikin

cikar shekara uku da samun yancin kai. Nnamdi Azikiwe ya zamo Shugaba (President) na farko a Nijeriya. Kundin na 1963 ya samu asali ne daga tsarin "Westminster". An yi amfani da shi har zuwa juyin mulkin soja na farko a shekarar 1966 inda aka kifar da gwamnatin farar hula ta farko, kuma aka yi watsi da kundin tsarin mulkin na demokaraɗiyya na farko a Nijeriya.

A lokacin wannan juyin mulkin an kashe Sir Abubakar Tafawa Ɓalewa Prime ministan farko da Sir Ahmad Bello Sardaunan Sakkwato premiyan Arewa da su Akintola premiyan Kudu ta yamma. Bayan kashe waɗannan bayin Allah, Ironsi ɗan kabilar Igbo ya zamo Shugaban ƙasa na soja na farko. Wannan ya haifar da "counter-coup" wadda a ƙarshe ƙasar ta faɗa cikin yaƙin basasa wanda Ojuku yace sai a barsu su ƙirƙiri ƙasar su ta BIAFARA. Wannan yaƙi anyi shi daga 1966 zuwa 1970 kuma ya haddasa mutuwar yan ƙasa masu ɗunbun yawa. Wannan "counter coup" ya samar da Gawon a matsayin Shugaban ƙasa na soja na biyu a Nijeriya, daga 1966 zuwa 1975 In ban manta ba.

Kundin shekarar 1979

Janar Murtala Ramat Muhammad ne ya yiwa Gwamnatin Gawon juyin mulkin da babu zubar da jinin kida ƙadangare a ciki, saboda wasu dalilai na zalunci ga yan ƙasa. Shi kuma bai daɗe ba shima aka kifar da shi tare da kashe shi a cikin wani coup da ba yi nasara ba. Sojoji sun naɗa OBASANJO shugaban ƙasa wadda shi kuma ya miƙa mulki ga farar hula.

Wannan kundi ya haifar da tsarin Junhuriyya ta biyu a Nijeriya. Kundin yayi watsi da tsarin "Westminster" mai tsarin firemiya, ya ɗauki tsarin shugabanci irin na Amurka mai Shugaban ƙasa da yan ƙasa suke zaɓa kai tsaye. Domin gujewa abinda ya faru a Junhuriyya ta farko, wannan kundi ya kafa dokar cewa duk wani "party" sai ya sami goyon bayan kaso biyu cikin uku (2/3)1 na duk jihohin Nijeriya kafin ya kafa mulkin shugabancin ƙasa. Kuma dai kundin ya tabbatar da "Cabinet of Nigeria" mai wakili a ƙalla ɗaya daga kowacce nahiya. Wannan zai daɗa tabbatar da Gamaiyya cikin tsarin sha'anin ƙasa.

Kundin shekarar 1993

Wannan kundi ya haifar da tsarin Junhuriyya ta uku a Nijeriya. Ya kamata ace wannan kundi ya mayar da Nijeriya kan turbar Demokaraɗiyya amma gaza aiwatar da shi ya hana. Saboda haka Sojoji suka ci gaba da iko a ƙasar har zuwa 1999 lokacin da suka miƙa mulki ga zaɓaɓɓen Shugaban ƙasa na farar hula. Amma kafin nan an samar da wani kundin a shekara ta 1995 wadda GENERAL Sani Abacha ya jagoranci sabunta shi, sai mutuwar GENERAL kwatsam a 1998 tasa ba a iya aiki da shi ba.

Kundin shekarar 1999

Shi kuma wannan kundi ya haifar da tsarin Junhuriyya ta huɗu a Nijeriya gamammiyar ƙasa mai tsarin mulkin demokaɗiyya. A ciki aka yi bayanin sashin babban garin Abuja a matsayin cibiyar gudanarwa da ragowar manyan garuruwan duk Juhohi 36, da kuma ƙananan hukumomi 774. A ciki dai aka fayyace ɓangarorin yin Dokoki, dana Zartarwa da na kula da Shari'a, tare da fayyace aikin kowanne da kuma

banbancin aiyukan Juhohi dana ƙananan Hukumomi. Ikon yin Dokoki an sanya shi ƙarƙashin kulawar gidaje biyu watau Majalisar Dattijai "Senate" da Majalisar Wakilai "House of Representatives"

Wannan kundi ya sha ƙare-ƙare da rage-rage tun daga samuwarsa kawo wannan lokaci, 2011, 2017, 2023, wadda har yanzun nan akwai bukatar sake duba shi domin kawo sauye-sauyen da jama'a suke buƙata.

Idan muka lura da kyau, zamu ga cewar kundin tsarin mulkin Nijeriya littafi ne ƙwaya ɗaya wanda ya sha canje-canje da sabuntawa daga lokaci zuwa lokaci. Saboda haka sai yakasance babu wata turba ƙwaya ɗaya da ake bi domin kaiwa ga gacin ci gaban al'umma.

3) Me wannan kundin na 1999 na ƙarshe ya ƙunsa?

Don ƙarin bayani duba cikakken Kundin a www.nigerian-constitution.com (NIGERIAN CONSTITUTION 1999).

Ya ƙunshi Dokoki ko ƙa'idoji daga lamba 1 zuwa lamba 320 amma wasunsu suna da yaya ƙarƙashinsu, tare da ƙarin bayanai a ƙarshensa.

A yanzu mun ciro kaɗan daga cikin muƙaddimar sa ne, kamar yadda take da Turanci, tare da Doka ta 1, 1(1), 1(3), 10, 33(1), 34(1), 38, 38(1) domin bayani da ta'aliƙi cikin harshen Hausa:-

Citation,

CONSTITUTION OF THE FEDERAL REPUBLIC OF NIGERIA.

"WE the people of the Federal Republic of Nigeria: HAVING firmly and solemnly resolved: TO LIVE in unity and harmony as one indivisible and indissoluble Sovereign Nation under God dedicated to the promotion of inter-African solidarity, world peace, international co-operation and understanding: AND TO PROVIDE for a Constitution for the purpose of promoting the good government and welfare of all persons in our country on the principles of Freedom, Equality and Justice, and for the purpose of consolidating the Unity of our people: DO HEREBY MAKE, ENACT AND GIVE TO OURSELVES the following Constitution:....."

1. Supremacy of the Constitution
1(1) This Constitution is supreme and its provisions shall have binding force on all authorities and persons throughout the Federal Republic of Nigeria.

1(3) If any other law is inconsistent with the provisions of this Constitution, this Constitution shall prevail, and that other law shall to the extent of the inconsistency be void.

10.Prohibition of State Religion.

The Government of the Federation or of a State shall not adopt any religion as State Religion.

33.Right to life

(33)(1) Every person has a right to life, and no one shall be deprived intentionally of his life, save in execution of the sentence of a court in respect of a criminal offence of which he has been found guilty in Nigeria.

34.Right to dignity of human person

(34)(1) Every individual is entitled to respect for the dignity of his person, and accordingly –
(a) no person shall be subject to torture or to inhuman or degrading treatment;
(b) no person shall be held in slavery or servitude; and
(c) no person shall be required to perform forced or compulsory labour.

38. Right to freedom of thought, conscience and religion
(38)(1) Every person shall be entitled to freedom of thought, conscience and religion, including freedom to change his religion or belief, and freedom (either alone or in community with others, and in public or in private) to manifest and propagate his religion or belief in worship, teaching, practice and observance.

_ End of citation.

Ta'aliƙi kan Muƙaddimar kundin shekarar 1999:

Tun daga farkon rubutun cikin kundin "Nigerian Constitution 1999" aka fara zazzago ƙarya.

CEWAR: "(WE the people of the Federal Republic of Nigeria: HAVING firmly and solemnly resolved:.....)" - Mu mutanen Junhuriyar Nijeriya, Mun yi matuƙar yadda da yanke shawara ta gaskiya cewar:....." Wannan magana ƙarya ce. Idan a yau ka ɗauki ƙididdiga (survey) na jama'ar dake cikin kasar da ake kira Nijeriya, ka tambaye su cewar - ko da yawunku aka rubuta waɗannan saɗarorin na farkon kundin gudanar da ƙasar Nijeriya? Zaka sami cewar 99% basu san lokacin da aka zauna aka yi haka da su ba. Kai ko wakilan su, ba su san wannan Magana ba. Tsofaffinsu da matasansu.

Shaida kan wannan kuwa shine irin ƙoƙarin da ɣan BIAFARA da ODUDUWA suke tayi cewar sai a basu yankin su ya ci gashin kansa a matsayin ƙasa mai cikakken iko. Ko mun manta da yaƙin basasa ne? Me yasa muke yaudarar kanmu?

CEWAR: "Sovereign Nation under God" - Ɣantacciyar ƙasa ƙarƙashin "God". Wanne God ɗin? Allah ko Yesu Almasihu ko Cineke ko ..... ko .....? Wannan magana ma ƙaryace domin ta saɓa da satsara ta 10 cikin kundin. Allah Shine mai Addini amma sunce basu yadda ƙasa ko jiha ta zama ƙarƙashin kowanne Addini ba. Sun kirayi (God)-Allah kuma sunce ba ruwansu da Shi, domin wanda ya ƙyamaci Addinin Allah, ya gujewa Allah kenan. Wannan wanne irin hauka ne?

Ina da yaƙinin mu yan Afrika ake so a yaudara. Domin Shugaban yaƙin ƙasar Amurka Hetegel ya fito ƙarara ya nuna cewar Amurka ƙasa ce da ta ɗauki Kiristanci a matsayin Addinin ta, ba Yahudanci ba, a'a Kiristanci wadda kullum suke canza ma'anoninsa.

CEWAR: "AND TO PROVIDE for a Constitution for the purpose of promoting the good government and welfare of all persons in our country on the principles of Freedom, Equality and Justice,....." - Kuma a samar da wani kundi domin aiwatar da shugabanci nagartacce tare da walwalar kowa da kowa a ƙasar mu bisa ƙa'idar yanci, daidaito da adalci..... La'akari da abinda ke gudana yau a cikin Nijeriya, kowa yasan wannan magana ƙarya ce.

Menene albashin yan siyasa, menene albashin gama garin ma'aikaci a gwamnati da kamfanoni? Kuna da aure kowa yana da aure, kuna da yaya kowa yana da yaya, yadda kuke ci kuke sha haka kowa yake yi. Idan aka kwatanta aikinku kan sikelin adalci, bai ɗara na masinjan dake sharar ofis ba. Domin rayuwa gabaɗayanta cuɗeni in cuɗeka ne.

Game da ɓangarorin yan sanda da kotuna kuwa, watau "Judiciary" kowa ya zama mai binciken sa da nazarinsa da kansa. Duk da cewa har kullum ba a rasa masu gaskiya da adalci da amana cikin al'umma, amma dai abinda ya yi ƙaranci kenan shi yasa muka tsinci kanmu cikin halin da muke ciki. Kullun kukan cin hanci da rashawa ake yi cewa an kasa dainawa, amma baƙin cin hanci da rashawa ya ƙare ga can sama ta yadda ake wadaƙa da dukiyar Al'umma "Public Fund and Wealth".

A tsari na gaskiya ana zaɓen Shugabanni domin jin daɗin Al'umma da walwalarsu ne. Amma tunda ake mulkin siyasa a Nijeriya, sai ya kasance azzuluman Shugabanni ake zaɓa waɗanda suka yi shigar 'ungulu da kan zabo' kuma suke ɗorawa Al'umma baƙar wahala kan wahala. Kullum cewa muke jiya tafi yau kyau. Wannan wacce irin musifa ce? Kenan "Nigerian Constitution" ƙarya ne. Wai an kori kare daga gindin ɗinya don a sha.

CEWAR: "DO HEREBY MAKE, ENACT AND GIVE TO OURSELVES the following Constitution:....." A yanzu nan mun, zartar da dokar baiwa kanmu wannan Kundi:....., Kanku, ku su wa?

Ba dai dukkan ɣan Nijeriya ne suka yadda da wannan magana ba! Ko kun ari bakin mutane ne kun ci musu albasa? Wallahi zamu tsaya daku gaba ga Zatin Allah za kuyi bayani.

Duk da cewa akwai abubuwa da dama cikin Kundin masu kyau, idan akayi la'akari da yarjejeniya ta zamantakewar lafiyar Al'umma baki ɗaya. Amma dai akwai tubka da warwara sannan wannan Kundi bai yiwa mu Musulmai adalci ba.

Doka ta Ɗaya:

1 Dokar ƘOLI

1(1) Wannan kundi shine KUNDIN DOKA ta ƘOLI kuma ya zama tilas (kasancewarsa hakan) akan ko wacce irin DOKA da kuma JAMA'AR Junhuriyar Nijeriya.

Ta'aliƙi:

Mu a tsarin mu na Musulunci, babu wata doka ta ƙoli (Suprême) face Dokar Allah. Saboda haka kace Kundin tsarin mulkin Nijeriya shine bisa Dokokin Alƙur'ani, Wallahi ƙarya kake, ba a haifi uwarka ba, bare ubanka.

Shi yasa nake mamakin wai da Musulmai kuwa aka rubuta wannan iskancin?

1(3) Idan wata doka taci karo da dokokin cikin wannan kundi, to dokokin wannan kundi sune gaba, kuma waccan dokar, da taci karo da shi, ta zama ɓatacciya (ba za a yi aiki da ita ba).

Ta'aliƙi:

Lokacin da Turawan mulkin mallaka suka ci mu da yaƙi sai suka kashe mana shugabanni, suka kori wasu daga fadar su, sannan suka dakatar da aiki da Dokokin mu na Islam. Yanzu sun barmu amma mun kasa gyarawa. Kuma Allah Yana kallonmu.

Doka ta Goma

10 Hana ɗabbaƙa wani Addini ɗaya a ƙasa duka ko wata Jaha.

Ba'a yarda Gwamnatin Tarayya ko ta Jaha, ta ɗauki wani Addini a matsayin Addinin ta ba.

Ta'aliƙi:

Idan har kowa yana da yancin yin Addininsa a Nijeriya, me yasa za a hana kafa 'State Religion', inda mafi yawan jama'a suka zaɓi hakan? Wannan kuma ya saɓa maganar muƙaddimar wannan kundin (FREEDOM, EQUALITY, JUSTICE) da kuma doka ta (38).

Ko waɗanda suka rubuta wannan kundin Arna ne, babu ruwansu da kowanne Addini? Ko kuma ba su san menene Addini ba?

Kafa 'State Religion' ba shi zai kallafawa duk wanda yake cikin wannan State karɓar wannan Addini a matsayin Addininsa ba. A'a kawai dai dole ya yi biyayya ga wasu ƙa'idojin zamantakewa. Idan kuma ba zai iya ba, sai ya koma State ɗin da yaga yafi dacewa da shi. Nijeriya tana da faɗi.

Doka ta Talatin da uku

33 Yancin Rayuwa.

(33)(1) Kowanne ɗan ƙasa na da yancin ya rayu, babu kuma wanda za a salwantar da rayuwarsa da niyya face sai dai idan wata dokar kotu ce ta yanke hukuncin hakan saboda laifin da mutum yayi wadda ya cancanci hakan a Nijeriya.

Ta'aliƙi

Haka ne, ya kamata kuma ya zama wajibi kowa ya sami cikakken yancin rayuwa. To amma duba da yadda Boko Haram da Fulani Bandits suke yin kan me uwa da wabi wajen kashe al'umma da sace su sai an biya kuɗin fansa kuma Hukuma ta siyasa, sojin ƙasa, sojin sama, sojin ruwa, DSS, ESS, FSS da kowacce tsiyar, sun kasa magance wannan al'amari, kasan cewar kundin tsarin mulkin Nijeriya KARYA ne.

Allah Ya jiƙan GENERAL SANI ABACHA. Yace "Babu wata tsiya da za ta faru a cikin ƙasa, face gwamnati ta magance ta cikin awa 24. Idan kuwa ba ta yi ba, to tana da hannu a ciki". Soja ne ya faɗa ba Ni ba.

Doka ta Talatin da huɗu

34. Yancin kare masa mutunci.

(34)(1) Kowanne ɗan ƙasa yana da hakkin kariya ta mutuncinsa a matsayinsa na ɗan ƙasa, kamar haka:

a) Babu wani mutum da za a azabtar da shi ko wulakanta shi kamar dabba.

b) Babu wani mutum da za a riƙa a matsayin bawa ko a kallafa masa bautawa (wani mutum).

c) Babu wani mutum da za a tilastawa/matsantawa aikin ƙarfin da ba zai iya ba (domin mugunta ko horo).

Ta'aliƙi

Wannan ma haka abin yake sai dai ina masu kare dokar, ina masu yin Shugabanci domin al'ummar su? Suka bari Fulani Bandits suke sace Mata masu aure katangaggu tare da yin layi kan kowacce. Suka bari waɗanda aka sace suke kwana cikin dazuzzuka ko mayafi babu, ake ɗanɗana musu azabar yunwa da tafiya da rashin kulawa da lafiyarsu. Ina waɗanda aka baiwa AMANAR Jama'a hakkin kulawa da su suke, sa'ad da bandit zai jefawa karensa ɗan jinjirin da wacce aka kama ta haifa domin karen ya cinye shi? Allah Ya Isa. A kwai wulaƙanta ɗan Adam ɗin da yafi wannan?

Saboda haka "Nigerian Constitution 1999" ƙarya ce tsagwaronta.

Doka ta Talatin da takwas

38 Yancin Tunani, Aƙida da Addini.

38(1) Kowanne mutum yana da yanci da damar yin Tunani, samun Aƙida da yin kowanne irin Addini, ba tare da tsangwama ba. Yana kuma da yancin canza Addininsa zuwa wani Addinin. Haka yana da yancin yin Addininsa a fili shi kaɗai ko cikin jama'ar da suke da Addini iri ɗaya dashi, da da'awa da koyar da shi (wannan Addinin nasa).

Ta'aliƙi:

Mu Addininmu ya Shar'anta mana dole muyi aiki da SHARI'A! Shin yanzu akwai wanda zai hana mu? Babu, saidai wanda ba ya son zaman lafiya. Wannan kuwa a yanzu zai ci ubansa la'ada waje, ko Musulmi ne ko ba Musulmi ba!

Sannan Dokokin Addinmu sun hana mu yin ridda. Saboda haka duk wanda ya bar Musulunci, za a bashi tsawon kwana uku ya tuba ya dawo. Idan ya ƙi, za a binciki lafiyar sa ko ya sami taɓin hankali ne. Idan haka ne hukuma za ta ci gaba da ba shi magani har ya warke. Idan kuma lafiyarsa lau, to kisa shine hukuncinsa. Ko kuma ya sulale ya bar ƙasar domin ragowar Al'umma za su ɗauke shi MUNAFUKI.

Abinda muke kira ga Musulmai shine su yi ƙoƙarin hanuwa daga dukkan abinda Allah da ManzonSa suka hanesu gaba ɗaya, domin kada haddi ya hausu, sannan su yi ƙoƙarin aikata abinda aka umarce su da aikatawa gwargwadon hali. Su kuma arnan cikinmu su yi ƙoƙarin mutunta dokokinmu da al'adunmu ko ba komai sa zauna lafiya domin gudun 'jungle Justice' daga gama-garin mutane.

Misali Musulmai suna kan yin sallar su ta Juma'a wata ƙadangariya fandƒararriya ta fito rabinta tsirara tace sai ta wuce ta gabansu. Itama tasan tsokana take yi.

Ko kuwa haka kawai wani ya zagi Manzonmu a gabanmu ko ya ƙona mana Alƙur'ani ko ya yayi najasa akansa da gangan domin wulaƙanta Addinmu, to wallahi sai inda ƙarfinmu ya ƙare. Wannan Aƙida ce ga duk wani Musulmi babba da yaro, mai Imani, hankali da ilimi.

Kowa yayi Addininsa ba tare da tsangwama ko tsokana ko tozarta ƙa'idojin wani Addinin saɓanin na mutum. Haka sai a zauna lafiya! Wai zabi sunga makaho.

4) Ina Mafita?

Da fari menene matsalolin?

Matsalolin sune kamar haka:

1) Ba kowa ne ya yarda da abinda ke cikin wannan kundi ɗari bisa ɗari ba.
2) Ba a iya aiwatar da Tsarinsa yadda ya dace
3) Ba a iya ba shi kariyar da ta dace.
4) Shugabanni sunyi biris da jin ko sauraron buƙatun talakawa.
5) Shugabanni na kawo Tsare-Tsare da ke daɗa jefa Talaka cikin ƙuncin Rayuwa, rusa tattalin arzikinsa da rusa ƙarfi ko darajar kuɗin ƙasarsa.
6) Shugabanni sun kasa Tattalin arzikin ƙasa ta yadda duk da arzikin Nijeriya, ake ciyo bashin Bankin Duniya mai tattare da ruwa da ƙa'idojin da suke jefa Talaka cikin musifa.
7) Shugabanni sun kasa samar da Tsaro ɗorarre
8) Barin ci gaba da wulaƙanta yan Nijeriya da Bandits da Boko Haram suke yi.
9) Barin ci gaba da sace mana albarkatun ƙarƙashin ƙasa da "Clandestin Syndicate" sukeyi a Sambisa da Zamfara da Katsina da ragowar sassan Nijeriya inda bincike ya tabbatar cewa akwai waɗannan ma'adanai.
10) Mayar da Jami'an Tsaron Ƙasar Nijeriya da su da babu ɗaya, kai ka ce babu Gwamnati a ƙasar!
11) Ƙasa samo bakin zaren warware duk waɗannan matsalolin.

Yanzu munji matsalolin to ina mafita?

Ƙarin bayani domin nemo mafita:

Kamar yadda marigayi GENERAL Sani Abacha (Allah Ya yi masa Rahama) ya faɗa cewar:

"Babu wata ɓarna ko tsiya da za ta faru a cikin ƙasa, face gwamnati ta magance ta cikin sa'o'i 24. Idan kuwa ba ta yi ba, to tana da hannu a ciki".

Fassarar wannan maganar shine duk iskancin da ake yi cikin ƙasa da hannun Gwamnati. Idan babu hanun wasu daga cikin Gwamnati, to da akwai hannun wasunsu.

Lokacin da Shugaban Kasa Jonathan yake kan mulki, ai ya ce akwai Boko Haram a Villa. Yana nufin akwai "representative" wakilansu a kewaye da shi duk da bai sansu ba. Kaji gaskiyar "Innocent President". Saboda haka gyaran babba ne. Akwai Matsala.

Sannan Shugaban ƙasar Nijar na wannan lokacin wanda soja ne, yayi wata magana kwanakin baya inda yace: "ashe ban sani ba Nijeriya ruɓaɓɓen kifi ne wadda ruɓewarsa ta fara tun daga kansa har jelarsa". Wannan ba sai an fassara maka ba.

Ya kamata mu waye, aikin ƙungiyar Boko Haram a Nijeriya ba domin MUSULUNCI ba ne, a'a aiki ne na waɗancan "Clandestin Syndicate" domin biyan wata buƙata ta su. Suna yin amfani da ƙungiyar da suka fahimta tana da tsatstsauran ra'ayi ne. Haka suma Fulani Bandits. Su kuma waɗannan suna amfani da su ne domin baƙin jahilci su.

Idan kun lura da idon basira, za ku ga duk inda ake wannan ɗauki ba daɗin, akwai wasu ma'adanai ƙarƙashin guraren wadda waɗannan Ɓarayi na waje da cikin gida suke kwasa.

Abin tambayar shine me yasa sai sun kashe jama'a sun koresu daga guraren kafin su sace dukiyar ƙarƙashin ƙasar gurin?

Yanzu ance an kawo sojojin Amurka domin tsaro, to an daina boko Haram ko Fulani Bandits? A'a wasu sabin ɓarayin aka kawo domin daɗa hargitsa Nijeriya tare da kwashe albarkatun ta. Yanzu za a yi satar "proper". Lokaci ne kawai zai nuna. Duba ga irin halin da Amurka da Isra'ila suka jefa wasu sassan Duniya cikin masifar yaƙi, kisa na zalunci da wawashe albarkatun man fetur da sauransu, bai kamata ko kaɗan kusantarsu ba, har a nemi wani abu a gurinsu. Ba su mutunta yancin Ɗan Adam. Duk abinda za su faɗa ƙarya ce. Kowa yana ganin abinda yake wakana a gabas ta tsakiya da Venezuela da Greenland da sauransu.

MAFITAR:

1) Komawa ga Allah gaba ɗayanmu. Dole mu daɗa gyara zukatanmu ɗaiɗaikunmu tare da Addu'o'i ga Allah SWT domin warware mana waɗannan matsaloli ta hanyar da muka sani da wadda bamu sani ba.
2) Tashi tsaye domin aikin da zai kawo mana canjin na gaskiya.
3) Rage kwaɗayi da son duniya tare da tuna Lahira koda yaushe domin canne Matabbaci na har Abada.
4) Haɗa kan manyan mu na daga Malamai, masu hannu da shuni, da masu shugabanci.....

5) Kula matuƙa da tarbiyyar matasanmu. Ba kowanne irin shirme za a bar yara su kwaikwaya ba na daga ɗabi'ar wasu mutanen can. Dole Hisba ta sake ɗamara.
6) Neman sake sabunta "Constitution" ta hanyar "referendum" raba gardama (ta jin ra'ayin talakawan ƙasa) domin cire abinda bai dace ba da ƙara abinda ya dace, idan har zamu zauna ƙasa ɗaya. In ba haka ba kuwa sai a yi "Confedaration" inda kowa zai ci gashin kansa duk da cewa dai za a yi zama irin na ƙawance tsakanin ɓangarorin uku ko huɗu.
7) Dole a kawar da sansanin sojojin Amurka daga Nijeriya.

5) Kammalawa

Alhamdu lilLahi rabbil 'alamiin.

Bldr. Ibrahim Muhammad Ɗankyauri

4 ga Muharram 1448 /// 20/06/2026